POETIC WEDNESDAYS initiative





Yanar Gizo

Kundin labarai da waƙoƙi na yan mata

Hausa Version

Tattarowa da Tacewa daga **Salim Yunusa**

Luminate
Building stronger societies
Hadis
Habiba Dangana Foundation
Giving a head Start in life

Gabatarwa

Samuwar yanar gizo da kafafen sada zumunta ya haifar da sabuwar ƙarni ga matasa, musamman Najeriya. Ya buɗe damarmakin da babu su, kusanto da nesa ya zama a tafin hannu, saukaka samun ilimi, damar bayyana ra'ayoyi, tare da samar da sabbin hanyoyin ƙulla zumunta. Su ma mata matasa ba a bar su a baya ba, amma ta wani ɓangare kuma bayyana raayi na zuwu da ƙalubale saboda yadda cin zarafi, hantara, da danniya ke ƙara bayyana a yanar gizo.

Amfani da yanar gizo a Najeriya musamman ga mata duk da yadda su ke ratsa sarkakiyar ƙalubale daga Zamantakewa, al'ada har ma da fasaha. Duk da hakan ba sababbi bane, tsofaffin matsalolin ne da ke cikin al'umma, madadin yanar gizo ta inganta su sai ta ƙara taɓarɓare su.

Rahoton da State of Online Harms ya fitar shekarar 2024 ya nuna cewa kashi 58 cikin 100 na mata a Najeriya sun taɓa fuskantar wani nau'i na cin zarafi a yanar gizo, yayin da miliyoyin mutane ke fuskantar cin zarafi, kalaman ƙiyayya, da tilastawa ta hanyar Online. Ba wai an kirkiro lambobi ba ne kawai, rayuwar tsangwama ta zahiri ce da ke sanya mata janyewa, ko yin shiru a yanar gizo.

Hakan ya sa mata matasa da dama ke kasancewa cikin taka-tsantsan yayin bayyana ra'ayoyinsu a yanar gizo. Idan mace ta Faye nuna kanta sai a fara bin ta da tambayoyin da su ka wuci gona da iri, haka zalika faɗin ra'ayi na iya ja mata cin zarafi daga wa'inda su ka saɓa ma raayinta. Saboda haka, wasu mata ke ganin laɓewa da yin shiru ne hanyar kare mutuncinsu.

Killace kansu da su ke yi ya rage musu damar ci gaba da rayuwa kamar kowa, a matakin sana'a, har ma da harkoki da jama'a. Rashin tofa albarkacin bakinsu ba ya sa ra'ayoyi da dama ba su wanzu ba, sannan tattaunawa tsakanin al'umma ya taƙaita, hanyoyin cin zarafi a yanar gizo na ƙara tsamari duk don rashin ɗaukan mataki. Bayan cyberbullying da tsangwama, sabbin barazana kamar yi ma mace taron dangi, fallasa bayanan sirri (doxing), da kirkirar hotunan bogi ta hanyar AI suna ƙara bayyana. Abubuwan da aka tsara domin ƙulla zumunci ya zama silar zalunci da danniya saboda ƙarancin wayewa akan dokoki da dabarun kare kai. Wannan ya sa yin amfani da fasaha cikin gaskiya da amana tare da kiyaye hakkin dan adam ke da matuƙar muhimmanci, wanda shine tsarin da aka kafa yanar gizo, watau ba wai tulin rubuce-rubuce ba sai a tsayayye tsari da ya bayar da damar bayyana ra'ayoyi.

Kundin na ya tattaro muryoyin mata matasa daga Kaduna da sauran Arewacin Najeriya, in da su ka bayyana yadda suke rayuwa a sararin yanar gizo. Sun taɓo abubuwan da ke faruwa na kusa da na nesa, sun tabo hatsarin da ke tattare da bayyana ra'ayoyi, amana da cin amana. Wasu sun iya dakewa su kwaci kansu. Yayin da wasu ba su iya yi ba, amma duk amon muryarsu Akan yadda ba a so suna bayyana ra'ayoyinsu da kuma kira da a dinga ba mata murya.

Adabi ke sa tarihi ya yi tsayin daka, hanya ce ta adana abubuwan da ake yawan watsi da su musamman abun da al'umma ke ganin "iyakarsa yanar gizo kawai," zai nuna tasirinsu a rayuwa. Adanlbi kan sauya abubuwan da mutum ya fuskanta shi kaɗai ya sa gama garin mutane su fahimta, yana ba da murya, yana kuma fito da abin da aka ɓoye.

Wannan kundi ya zo a daidai lokaci da ake matukar bukatarsa. Yayin da amfani da intanet ke ƙaruwa, ba batun shiga kawai ake yi ba, har da tsaro da adalci.

Kundinbai tsaya akan matsalolin ba maeak, ya bayyana dabarun da za a bi a samu sauyi, ta hanyar bayyana cin zarafi da dabarun magance shi, marubutan suna samar da wata duniyar yanar gizo mafi aminci, inda mata za su iya shiga gaba-gadi ba tare da tsoro ba.

An fassara kundin zuwa Hausa, domin tabbatar da cewa mata da dama za su iya ganin kansu a ciki, sakon ya shiga lungu da saƙo, har mata su dena jin tsoron bayyana ra'ayoyinsu a kafafen sadar da zumunta.

An samu nasarar wannan aiki ne da tallafin Hadis Foundation da Luminate, tare da Poetic Wednesdays Initiative, da kuma gudunmawar masana da abokan aiki da suka tabbatar da inganci wannan aiki.

Abin da ke hannunku ba kawai tarin kalamai ba ne. Shaida ce, tarihi ne, kuma kira ne zuwa ga aiki. Idan kun gani ku ɗauki abun da kuka karanta da muhimmanci sannan ku yi aiki da shi.

Salim Yunusa
Edita, Kundin Yanar Gizo

Game da kungiyar Poetic Wednesdays

Poetic Wednesdays Initiative ƙungiya ce ta adabi mai zaman kanta, wadda ba ta gwamnati ba ce kuma ba ta siyasa ba ce, wadda ta mayar da hankali kan matasa domin inganta ƙirƙira, fikra, rubutu, ilimi, da damar bayyana ra'ayi musamman a Arewacin Najeriya. Ƙungiyar tana gudanar da ayyukanta ta yanar gizo da kuma a fili, inda ta samar da dandali mai ƙarfi ga matasa marubuta da masu fasaha domin haɗuwa, bunƙasa basirarsu, da shiga tattaunawa mai ma'ana ta hanyar adabi.

Da hangen nesa na ƙarfafa matasa su gano tare da amfani da baiwar adabi da suke da ita, Poetic Wednesdays na amfani da fasahar ƙirƙira a matsayin hanya ta wayar da kai da fafutuka kan manyan matsalolin al'umma. Ƙungiyar tana bayar da gudummawa wajen bunƙasa ingantaccen ilimi da ƙirƙire-ƙirƙire, daidai da manufofin ci gaban duniya.

Ta hanyar horaswa, tarukan adabi, shirye-shiryen jagoranci da horaswa, da kuma hulɗa ta kafafen dijital, Poetic Wednesdays na tallafa wa sababbin hazikai, inganta al'adar karatu da rubutu, tare da wayar da kai kan ƙalubalen zamantakewa. Tsarinta na bai wa kowa dama yana ƙarfafa amfani da Turanci da harsunan gida, wanda ke taimakawa wajen gina al'ummar adabi mai armashi da bambance-bambance.

Tun bayan kafuwarta, ƙungiyar ta taimaka wa dubban matasa ta hanyar shirye-shiryen horaswa, dandamalin ƙirƙira, da haɗin gwiwa na dabaru, inda take taimaka musu gano da bunƙasa baiwar adabinsu tare da bayar da gudummawa ga ci gaban ilimi da zamantakewa baki ɗaya.

Game da tsarin Yanar Gizo

Yanar Gizo wani tsari ne na bunƙasa ilimin dijital ta hanyar ba da labari, wanda marubuci kuma mai fafutukar habbaka adabi da ilimin dijital, Malam Salim Yunusa, ke jagoranta. Shirin yana maida hankali kan sauya bayanai masu rikitarwa da suka shafi amfani da fasaha cikin ɗabi'a, tsaron yanar gizo, da nagartaccen zama ɗan ƙasa na dijital zuwa labarai masu jan hankali da suka dace da al'ada da rayuwar matasa.

Ta hanyar haɗa rubutun ƙirƙira, ba da labari na dijital, da koyon haɗin gwiwa, Yanar Gizo na bai wa matasa, musamman 'yan mata da matasan yan mata damar fahimtar haɗurran da ke tattare da amfani da intanet, bayyana abubuwan da suka fuskanta, tare da inganta zaman aminci a yanar gizo.

Tsarin ya ginu ne a kan ayyukan da suka gabata na ilimin dijital ta hanyar ba da labari, ciki har da ƙirƙirawa da fassara littafin Rakiya zuwa Hausa, wanda ya yi amfani da labari wajen koyar da dabarun kare kai a yanar gizo.

Ta hanyar bitoci masu hulɗa da juna, mahalarta suna samun horaswa kan tsaron dijital, amfani da fasaha cikin ɗabi'a, da rubutun ƙirƙira. Daga nan sai su rubuta labarai na gaskiya da suka shafi matsaloli kamar cin zarafin mata a yanar gizo (OGBV), kare sirri, da amfani da intanet cikin alhaki. Ana tattara waɗannan labarai cikin kundin dijital, tare da gabatar da waƙoƙin spoken word, ziyartar makarantu, da shirye-shiryen hulɗa da al'umma domin faɗaɗa wayar da kai da sauƙaƙa samun ilimin.

Yanar Gizo na da burin sanya ilimin tsaron dijital ya zama mai sauƙin fahimta da kusanci da rayuwar matasa, ta hanyar sauya bayanan hukuma zuwa labaran da suka dace da abubuwan da matasa ke fuskanta a rayuwar yau da kullum. Shirin yana mai da hankali ne kan ɗaliban makarantar sakandare, ɗaliban manyan makarantu, da ƙungiyoyin matasa, domin ƙarfafa amfani da intanet cikin alhaki da kuma ingantacciyar shiga harkokin dijital.

Ana gudanar da wannan shiri tare da tallafin Hadis Foundation da Luminate, waɗanda gudummawarsu ke taimakawa wajen gudanar da bitoci, samar da abun ciki, fassara, da ayyukan wayar da kai, domin gina al'umma mai ilimi, alhaki, da juriya a duniyar dijital.

Godiya

Wannan kundin labarai ba zai samu nasarar kammaluwa ba da ba don tallafi da goyon bayan Hadis Foundation da Luminate ba, waɗanda suka yarda da wannan aiki tare da ɗaukar nauyin bitar horaswa, kundin labaran, da kuma fassarar kundin zuwa Hausa domin ya isa ga al'umma masu yawa, sakamakon muhimmancin amfani da fasaha cikin ɗabi'a da alhaki.

Ina miƙa godiya ta musamman ga dukkan matasan mata da suka bayar da gudummawa tare da rubuta labaransu domin wayar da kai da ilmantar da al'ummomin gaba masu tasowa.

Ina godiya ga Malam Fareed Ibrahim, Malam Aliyu Kutigi, Hajiya Zainab Idris, Malam Mohammed Yayandi Bayero, Malam Usman Karofi, Malam Habibu Galadima, da dukkan waɗanda suka bayar da gudummawa, goyon baya, da taimako wajen ganin wannan kundin ya tabbata.

A ƙarshe, ina miƙa godiya ta musamman ga matata abar ƙaunata, Nurse Khadija Bambale, saboda haƙuri, fahimta, da shawarwarin da ta bayar waɗanda suka taimaka wajen inganta wannan kundin. Kin sa kundin ya qara kyau, kuma kin sauƙaƙa mini hanyar ganin inganta shi.

Ga duk wanda ya karanta wannan kundi, ya yada shi, kuma ya fi amfani da intanet cikin hankali da kula saboda abin da ya koya daga cikinsa, ina matuƙar gode muku.

An fara wallafa wannan littafi a Nijeriya ta hannun

Poetic Wednesdays Initiative, Kano (2026)

Wanda ya tattara kuma ya gyara: **Salim Yunusa**

Zane, tsarawa da gyara shimfiɗa: **Aliyu Alhasasn Kutigi**

An kiyaye dukkan haƙƙoƙi. Dukkan wannan aiki yana ƙarƙashin dokar haƙƙin mallaka. Ba a yarda a ɗora, adanawa, sarrafawa, sake bugawa ko watsawa da wani sashe na wannan aiki ta kowace hanya ko wata kafa ba, ta lantarki ko ta na'ura, ciki har da ɗaukar hoto (photocopy) da rikodi, ko ta kowace hanyar adanawa da dawo da bayanai, sai da izinin rubuce daga mai wallafa a madadin mamallakin haƙƙin mallaka.

ISBN: 978-978-68-7621-4

Ana samun kwafin wannan littafi a Babban Laburaren Ƙasa na Nijeriya.

Jerin Abubuwan Ciki

Title Page - Yanar Gizo: A Collection of Digital Footprints by Young Women

Gabatarwa - Salim Yunusa	-	1
About Poetic Wednesdays Initiative	-	2
About Yanar Gizo Project	-	2
Godiya	-	3
Jerin Abubuwan Ciki	-	5
Kalmomi Da Ya Kamata Ku Sani a Yanar Gizo	-	6
Labari - Kwamen Sekhan	-	11
Labari - Karya Ta Kare	-	12
Poetry - Ya Ubangiji	-	13
Labari - Tsalle Daya	-	14
Poetry - Yayin Shiga Yanar Gizo	-	17
Poetry - Ke Mace ce	-	19
Poetry - Raunuka Marasa Hannaye	-	20
Poetry - Kawai Ni Mace Ce	-	21
Labari - Bakuwar Lamba	-	22
Hotuna	-	25

Kalmomi Da Ya ƙamata Ku Sani a Yanar Gizo

Accessibility: Tabbatar da cewa Fashar Zamani tana aiki ga kowa da kowa, misali amfani da umarnin murya ga mutanen da ba sa iya buga rubutu.
Accountability: Ɗaukar alhaki kan abin da ka yi a Yanar gizo.
Advocacy: Tsayawa ko goyon bayan matakai don sanya datar Yanar gizo ta yi araha ga kowa.
Algorithm: Jerin umarni da kwamfuta ke bi don nuna maka abubuwa a Yanar gizo, kamar bidiyo ko talla da ta yi zaton za ka so.
Anti-virus So ware: Shirin kwamfuta da ke kare kwamfuta daga ƙwayoyin cuta.
Artficial Intelligence (AI): Kirkirarriyar basira, na'urori/kwamfutoci da ke iya koyo, tunani, ko yanke shawara kamar mutane.
Artficial Superintelligence (ASI): Super Kirkirarriyar basira da ake hasashen nan gaba za ta fi hankalin mutane wayo; masana na ci gaba da nazari a kai.
Backup: Ajiyar madadin, ajiyar kwafin muhimman fayiloli a wani wuri dabam.
Automation: Aiwatarwa ta atoma kamfani da na'urori su yi ayyukan da mutane kan yi, kamar rarraba wasiku ko shara.
Bias: Son zuciya, nuna gefe ɗaya na labari ka bar sauran muhimman bangarori ko hangen nesa na wasu.
Building Trust Online: Gina amana a Yanar gizo, yin gaskiya da kirki don ƙulla abota.
Business Technology: Fasahar Zamanir kasuwanci, Fashar Zamani da ke taimaka a sayarwa ko ƙirga kuɗi.
Chatbot: Shirin kwamfuta da ke ta aunawa da mutane kuma yana amsa tambayoyi yanar gizo, kamar mataimaki na kama-da-gaskiya.
Clickbait: Kanun jan-hankali da ke sa ka danna mahadi ko labari, amma watakila ba gaskiya ba ne.
Cloud Storage: Ajiyar girgije, ajiye fayiloli a Yanar gizo don ka iya samunsu daga ko'ina matuƙar kana da Yanar gizo da bayanan shiga.
Coding: Koding, rubuta umarni da ke gaya wa kwamfuta abin da za ta yi.
Collaborative Tools: Kayan aikin haɗin gwiwa, manhajoji/shafuka da ke ba mutane damar aiki tare yanar gizo (misali raba fayiloli ko Google Docs).
Consent: Yarda nemi izini kafin raba hoton wani, bidiyo, ko bayanansa a Yanar gizo.
Content Modera on: Kula da abun ciki, tabbatar da cewa abin da ake wallafawa a Yanar gizo lafiya ne kuma ba ya cutar da wasu.
Context: Mahalli fahimtar cikakken labari kafin gaskata ko raba wani abu.
Cookies: "Kukis" ƙananan bayanai da shafukan Yanar gizo ke bari a kwamfutarka don tuna abubuwan da kake so ko wuraren da ka ziyarta.
Copyright: Hakkin mallaka, doka da ke kare ƙirƙira don kada a kwafa ba tare da izini ba.
Critical Evaluation: Tantancewa mai zurfi, duba bayani a hankali don sanin ko abin dogaro ne.
Critical Thinking: Tunani mai zurfi, taka-tsantsan kan abin da kake gani/karanta a Yanar gizo don tantance gaskiya.
Cultural Sensitivity: Hankali ga al'adu, girmama al'adu daban-daban yanar gizo.
Cyber Ethics: Ɗabi'un Yanar gizo, halayya nagari da adalci yanar gizo.
Cyber Hygiene: Tsa ar Yanar gizo, dabi'u kamar amfani da kalmomin sirri masu ƙarfi da guje wa shafukan da ba su da tsaro.
Cyber Threats: Barazanar Yanar gizo, kamar ƙwayoyin cuta ko masu kutse da ke iya lalata ko satar bayani.
Cyberbullying Preven on: Rigakafin cin zarafi a Yanar gizo, koyo yadda ake dakatar da mummunan hali yanar gizo.
Cyberbullying: Cin zarafi a Yanar gizo, cutar da wani ta saƙonni ko wallafe-wallafe.
Cybersecurity: Tsaron Yanar gizo, garkuwa da ke kare kwamfuta da bayanai daga miyagu.
Data Ownership: Mallakar bayanai, sanin cewa bayananka naka ne.
Data Plan: Tsarin data, kunshin mai ba da sabis don amfani da Yanar gizo na wani adadi da kudi.
Data Privacy: Sirrin bayanai, kare adireshi, lambar waya, da sauransu daga baki.
Data: Bayanai, lambobi, hotuna, ko kalmomi da kwamfuta ke amfani da su don koyo ko warware matsala.

Kalmomi Da Ya ƙamata Ku Sani a Yanar Gizo

Data-Saving Mode: Yanayin tanadin data, sai da ke rage cin datar Yanar gizo.
Deepfakes: Bidiyo ko hotuna na bogi da aka yi su kama da na gaske.
Deep Learning: Koyo mai zurfi, ɓangare na AI da ke koyo daga bayanai masu yawa kamar kwakwalwa.
Digital Accessibility: Sauƙin amfani da Fashar Zamani ga kowa, ciki har da mata, masu nakasa, da talakawa.
Digital Activism: Gwagwarmayar Fashar Zamani amfani da Yanar gizo don yada muhimman batutuwa da aiki tare don inganta duniya.
Digital Bias: Son zuciya na Fashar Zamani idan shafuka/kwamfutoci suna nuna bayani maras adalci.
Digital Campaign: Kamfen na Fashar Zamani yada muhimmiyar manufa ta Yanar gizo.
Digital Citizen: Dan ƙasa na Fashar Zamani mai amfani da Yanar gizo cikin kirki da tsaro.
Digital Citizenship: Ɗan ƙasanci na Fashar Zamani amfani da Yanar gizo cikin kirki, tsaro, da hikima.
Digital Collaboration: Haɗin gwiwar Fashar Zamani yin aiki tare yanar gizo.
Digital Content: Abun cikin Fashar Zamani bidiyo, hotuna, kiɗa, labarai, da sauransu.
Digital Crea vity: Kirkira ta Fashar Zamani zane, bidiyo, ko kiɗa ta manhajoji.
Digital Device: Na'urar Fashar Zamani waya, kwamfutar hannu, kwamfuta, da sauransu.
Digital Equity: Adalci a Fashar Zamani dama iri ɗaya ga kowa a Fasahar Zamani.
Digital Ethics: Ɗabi'ar Fashar Zamani ka'idojin amfani da Yanar gizo cikin adalci da alhaki.
Digital Footprint Management: Sarrafa sawun Fashar Zamani taka-tsantsan da abin da kake wallafa.
Digital Footprint: Sawun Fashar Zamani alamomin bayanai da kake bari a Yanar gizo.
Digital Impact: Tasirin Fashar Zamani yadda Fashar Zamani ke sauya rayuwa.
Digital Inclusion Programs: Shirye-shiryen haɗa kowa da Fashar Zamani tallafa wa kowa ya koyi Fasahar Zamani.
Digital Journaling: Rubutun ajanda na Fashar Zamani rubuta abin da ya faru ko ra'ayoyi ta manhajoji.
Digital Inclusion: Haɗa kowa a Fashar Zamani tabbatar kowa na iya amfani/koyo game da Fasahar Zamani.
Digital Literacy: Ilimin Fashar Zamani koyo amfani da kwamfuta, waya, Yanar gizo don nemo/raba/fahimtar bayani.
Digital Problem Solving: Magance matsala ta Fashar Zamani amfani da Fashar Zamani don gyara ko ingantawa a al'umma.
Digital Recycling: Sake sarrafa na'urori sake amfani ko zubar da su cikin tsaro.
Digital Reputation: Suna a Yanar gizo abin da mutane ke tunani a kanka bisa abin da kake raba.
Digital Responsibility: Alhakin Fashar Zamani sanin yadda ake yin hali yanar gizo da kare wasu.
Digital Safety Audit: Binciken tsaro na Fashar Zamani duba tsaron kwamfuta/manhajoji/asusu.
Digital Skills: Ƙwarewar Fashar Zamani buga rubutu, bincike, aika imel, da sauransu.
Digital Time Management: Sarrafa lokacin Screen daidaita Screen da wasa da hutu.
Digital Tools for Creativity: Kayan aikin kirkira na Fashar Zamani manhajoji don zane, kiɗa, bidiyo.
Digital Tools: Kayan aikin Fashar Zamani ƙalƙuleto, zane, ko wasannin koyo.
Disinformation: Bayani ƙarya da aka yada da gangan don ɓatar da mutane.
E-Learning Platforms: Dandalin koyo ta Yanar gizo shafukan da ke bayar da darussa.
Email Skills: Ƙwarewar imel rubuta da aika saƙonni yanar gizo.
Emotional Appeals: Kiran motsin zuciya labarai ko hotuna da ke tada ji sosai.
Emotional Resilience: Juriyar motsin zuciya koyon zama da natsuwa ko da an ba ka haushi a Yanar gizo.
Encryption Tools: Kayan aikin ɓoyewa maida saƙonni su zama lambar asiri.
Encryption: Ɓoyewa lambar asiri da ke kare bayani.
Entertainment Technology: Fashar Zamani na nishaɗi wasanni, fina-finai, kiɗa da Fashar Zamani ta ƙirƙira.
Ethical Behavior: Hali na ɗabi'a yin abin da ya dace a Yanar gizo, ba sata ko yaudara.
Ethical Hacking: Hakin ɗabi'a gano da gyara matsaloli don kare kwamfutoci daga miyagu.
Ethical Reporting: Bayar da rahoto cikin ɗabi'a faɗin gaskiya ba tare da cutar da wasu ba.
Ethical Use of Technology: Amfani da Fashar Zamani cikin gaskiya da adalci ba yaudara ko kwafar aikin wasu.

Kalmomi Da Ya kamata Ku Sani a Yanar Gizo

Ethics: Ɗabi'u ka'idojin abin da ya dace ko bai dace ba.
Fact-Checking: Tabbatar da gaskiya bincika ko abu gaskiya ne.
Fair Use: Amfani bisa doka amfani da aikin wani da izini ko yadda doka ta yarda.
Fake News: Labaran ƙarya wadanda ke iya yaudarar mutane.
Fake Profiles: Profayil ɗin bogi asusun da aka yi na karya.
Firewall: Garkuwar kwamfuta (Firewall) hana abubuwa marasa kyau shiga kwamfuta.
Hacking: Hakin kutse cikin kwamfuta ko tsarin kwamfuta. Masu hakin ɗabi'a na taimakawa su gyara matsalolin.
Hardware: Kayan jiki na kwamfuta Screen, madannai, linzami, da sauransu.
Healthy Screen Habits: Kyawawan dabi'un Screen yin hutu daga Screen don kiwon lafiya.
Identity Theft : Satar shaidar mutum wani ya yi kamar kai a Yanar gizo don ya sace abu.
Inclusion in Tech: Haɗa kowa a Fasahar Zamani Fashar Zamani ta amfani ga kowa, har da yara.
Information Overload: Cunkoson bayani yawan bayani a Yanar gizo da ke rikita kai.
Information Technology (IT): Fasahar Zamanir bayanai amfani da kwamfuta don warware matsala ko sauƙaƙa aiki.
Interactive Archives: Ayyuka masu mu'amala danna, motsa, ko buga don koyo.
Interactive Learning: Koyo ta mu'amala amsa tambayoyi/wasanni don fahimtar jigo.
Interactive Tools: Kayan mu'amala manhajoji da ke ba ka damar koyo ta wasa ko tambayoyi.
Internet Data: Data na Yanar gizo bayanan da ake tura/karɓa yayin amfani da Yanar gizo.
Internet of Things (IoT): Yanar gizo na Abubuwa fi lu, firiji, da dai sauransu suna haɗe da Yanar gizo.
Internet: Yanar gizo kamar babbar maktaba ce don magana, wasa, da koyo.
Keyboarding: Bugawa da madannai, buga kalmomi a kwamfuta.
Logical Reasoning: Tunani mai hujja, amfani da man ki da hujjoji.
Machine Learning: Koyon na'ura, kwamfuta na koyo da inganta kanta.
Media Influence: Tasirin kafofi yadda abin da ka gani a Yanar gizo ke shafar tunani/ayyukanka.
Media Literacy: Ilimin kafofin watsa labarai gane gaskiya ko yaudara a labarai/bidiyo/wallafe-wallafe.
Media Messages: Saƙonnin kafofi abubuwan da kake gani/ji da ke ba da labari ko ra'ayi.
Medical Technology: Fasahar Zamanir kiwon lafiya na'urori da ke taimaka wa likitoci.
Mindful Posting: Wallafawa da tunani yin tunani kafin raba hotuna/saƙonni.
Misinformation: Bayani mara daidai da aka yada ba da gangan ba.
Netiquette: Ne ke kyawawan halaye a Yanar gizo: ladabi, guje wa ɓatanci, girmama ra'ayi.
Offline Mode: Yanayin ba tare da Yanar gizo ba amfani da manhaja ba tare da Yanar gizo ba.
Online Collaboration: Haɗin gwiwa yanar gizo aiki tare ta Google Docs/hirar rukuni.
Online Communities: Al'ummomin yanar gizo rukunin ta aunawa kan abin da kowa ke so/ damuwa da shi.
Online Consent: Yarda tyanar gizo nemi izini kafin raba hoton/labarin wani.
Online Etiquette: Ka'idojin halayya yanar gizo zama mai girmamawa da kirki.
Online Feedback: Ra'ayi yanar gizo sharhi/shawara game da aikinka/wallafinka.
Online Harassment: Cin zarafi yanar gizo mummunar magana/cuta; gaya wa babba amintacce.
Online Libraries: Maktabobin yanar gizo shafukan karatu/bincike.
Online Manners: Ladabi yanar gizo godiya da kirki.
Online Portolio: Fayil ɗin ayyuka yanar gizo tarin mafi kyawun ayyukanka.
Online Predator: Maifarauta yanar gizo masu yaudarar yara/cutarsu; kada ka raba sirrika da baki.
Online Reputation: Suna yanar gizo abin da ake tunani a kanka bisa halayenka a Yanar gizo.
Online Research: Bincike yanar gizo nemo bayani mai amfani.
Online Safety: Tsaro yanar gizo taka-tsantsan, kada ka raba sirri, ka yi magana da waɗanda ka sani.
Online Threats: Barazanar yanar gizo masu son satar bayani/yaudara.
Online Workshops: Bitoci yanar gizo ajuzu/ taro a Yanar gizo don koyo ko raba ra'ayi.
Opera on Technology: Fasahar Zamanir aiki na'urori da ke taimaka wa masana'antu kera kaya.
Opinion vs. Fact: Ra'ayi da gaskiya gane bambanci.
Password: Kalmar sirri makullin asiri don kare asusunka; ka yi mai ƙarfi da haruffa, lambobi, da alamomi.
Personal Framework: Tsarin kai na ɗabi'a ka'idojin da kake bi don yin alhaki a Yanar gizo.
Personal Information: Bayananka na sirri, suna, adireshi, lambar waya; raba ga manya aminta u kaɗai.
Phishing Scams: Makircin phishing, wani na yi kamar banki/aboki don satar bayani; ka tambayi babba amintacce.

Kalmomi Da Ya kamata Ku Sani a Yanar Gizo

Phishing: Yaudara don a fito da sirrika kamar kalmar sirri/bayanan banki ta hanyar yi kamar wanda ka yarda da shi.
Piracy: Sata ta Fashar Zamani satar/raba fina-finai/waƙoƙi ba tare da biya ba.
Plagiarism: Kwafi ba da izini ba kwafar aikin wani ka ce naka ne.
Pop-Up Ads: Tallan da ke fitowa cak a Screen wasu na iya zama na yaudara ko ba su da tsaro.
Presentation Tools: Kayan gabatarwa manhajoji kamar PowerPoint don nuna ra'ayi da hotuna/kalmomi.
Privacy Settings: Saitunan sirri zaɓuɓɓukan tantance wa zai ga hotuna, wallafe-wallafe, ko bayanai.
Privacy: Sirri kare bayananka, kada ka raba da baki.
Product Technology: Fasahar Zamanir samarwa inganta kayayyaki kamar abinci/kayan wasa.
Propaganda: Farfaganda bayani na ƙarya/na gefe ɗaya don sa mutane su yi imani.
Public Wi-Fi Risks: Hatsarin Wi Fi na jama'a amfani a wuraren jama'a ba tare da kariya ba.
Public Wi-Fi: Wi Fi na jama'a Yanar gizo kyauta a wuraren jama'a; ba koyaushe yake da tsaro ba.
Respectful Communication: Sadarwa cikin girmamawa magana ba tare da cin mutunci ba.
Respecting Privacy: Girmama sirri kada a raba sirrin wasu ko bayanansu.
Responsible Sharing: Raba cikin alhaki yi tunani kafin wallafa.
Responsible Technology Use: Amfani da Fashar Zamani cikin alhaki da hikima da kirki.
Risk Assessment: Kimanta haɗari duba tsaro kafin saka bayani a wani shafi.
Role-Playing Games (RPGs): Wasannin kwaikwayo ka taka rawa a matsayin hali ka yi kasada tare da wasu.
Safe Browsing: Yawo cikin tsaro guje wa shafukan bogi/marasa tsaro.
Safe Wi-Fi: Wi Fi mai tsaro yana kare bayananka daga baki.
Safety Protocols: Ka'idojin tsaro kamar kada a danna mahaɗan da ba a sani ba, kada a yi magana da baki.
Scams: Zamba dabarun satar kuɗi ko bayani a Yanar gizo.
Screen Sharing: Raba Screen nuna Screennka yayin kiran bidiyo.
Screen Time: Lokacin Screen daidaita da wasa da hutu.
Search Engine: Injin bincike kamar Google don nemo bayani/hotuna/bidiyo.
Secure Websites: Shafukan Yanar gizo masu tsaro masu "h ps" da ke kare bayani.
Sharing Respectfully: Raba cikin girmamawa aika/buga abin da ba zai cutar da wasu ba.
Smart Device: Na'urar wayayya kamar waya/mai magana da ke amfani da AI.
Social Media: Kafofin sada zumunta Facebook, Instagram, da sauransu.
Source Credibility: Amincin tushe duba ko marubuci abin dogaro ne.
Software: Manhajoji umarnin da ke gaya wa kwamfuta abin da za ta yi (wasa, app, shiri).
Space Technology: Fasahar Zamanir sararin samaniya rokoki da tauraron dan'adam.
Spam: Saƙonnin banza saƙonni/imel da ba ka nema ba, kuma ba su da tsaro.
Stereotypes: Kinta u ra'ayoyin da ba koyaushe suke gaskiya ba game da abin da maza/yan mata za su iya ko ba za su iya ba.
Streaming: Yawo kai tsaye Screen/sauraro a Yanar gizo ba tare da sauke su ba.
Strong Passwords: Kalmomin sirri masu ƙarfi haɗa haruffa, lambobi, da alamomi.
Superintelligence: Hankali mai girma sosai kwamfuta mai wayo fiye da mutane, ana nazari a kanta.
Sustainability in Technology: Dorewar Fasahar Zamani amfani da Fashar Zamani ba tare da lalata muhalli ba.
Tech Upgrades: Haɓaka Fasahar Zamani ƙara sababbin sassa/shirye-shirye don inganta aiki.
Tech-Free Time: Lokaci ba tare da na'ura ba jin daɗin sauran ayyuka ba tare da Screen ba.
Technology Limits: Iyakokin Fasahar Zamani saita dokokin amfani da na'urori.
Technology: Fasahar Zamani kayan aiki kamar waya/kwamfuta da ke sauƙaƙa aiki, koyo, wasa, tafiya.
Transportation Technology: Fasahar Zamanir sufuri motoci, jirage, kekuna.
Troubleshooting: Neman matsala da gyarawa gano/gyara matsalolin kwamfuta/waya.
Trustworthy Content: Abun ciki abin dogaro bayani na gaskiya.
Trustworthy Source: Tushen abin dogaro shafi ko mutum mai bayar da sahihin bayani.
Two-Factor Authenthication (2FA): Tabbatarwa ta matakai biyu kalmar sirri da lambar waya don shiga asusu.
Typing Practice: A sayen buga rubutu koyo buga rubutu da sauri kuma daidai.
Two-Way Communication: Sadarwa ta bangarori biyu jayayya mai kyau inda kowa ke magana da sauraro yanar gizo.
Verification Tools: Kayan aikin tantancewa shafukan duba gaskiya da makamantansu.
Verification: Tantancewa duba ko abu na gaske ne/gaskiya (misali ko hoton an gyara shi).
Video Editing: Gyaran bidiyo gyarawa don su yi kyau ko su ba da labari.
Virtual Learning: Koyo ta Yanar gizo kallon darussa ko yin aiki yanar gizo.
Virtual Reality (VR): Kama-da-gaskiya saka tabarau na musamman ka ji kamar kana a wani duniya.
Wi-Fi: Wi Fi Fasahar Zamanir haɗa na'urori da Yanar gizo ba tare da wayar igiya ba.

Ni ɗaliba ce a jami'ar jihar Kaduna, kwata-kwata rayuwar yanar gizo ba ta gaba na don in na ga ana zagin mace a wajen Sam ba na tausayinta sai ma in ce ita-ta-ja, don a tunani na ballagaza ce.

A hankali na fahimci kafofin sadar da zumunta ma wata dama ce da mutum zai dinga wallafa labarai, bayyana raayin sa har ma kila kawo gyara a cikin al'umma. Hakan ya sa na fara wallafa labarai da raayoyinahar ma wani lokaci ƙawata Hauwa kan yi mun bidiyo ina rera wakokin da na rubuta in wallafa.

Shekaranjiya ina zaune da Hauwa karkashin bishiyar dalbejiya, sai ta ce na rera mata baitukan da na yi akan mahimmancin ilimin yƴa mace da barinta ta kai ga ƙololuwar nasara.

A nan ta fito da wayarta ta ce in zauna da kyau in rera

"sunana zainab, ni macece da ke da hakkin yin rayuwa kamar kowa, in yi ilimi in yi aiki, ba tare da aure ko al'ada ya hana ba…

Ko da na wallafa ban yi tunanin zai wuce mutane kalilan da ke bin shafi na ba, amma kafin awa ɗaya bidiyon ya samu mutane dubu biyar da su ka kalla, bloggers sun ɗaura shi a shafukansu suna yabon kalamains da fikirata. Abun da na yi tunanin nasara ce ashe ba nan gizo ke saƙa ba.

Sai da na shiga karanta raayoyin mutane da dare,

"Jaka yƴar neman suna" ne kwamen din farko da ta fara katari da shi, hannu na rawa ta yi ƙasa

"kin amso kwangila ne kema, arniya kawai"

"kin yi kwantai kina neman yƴan uwa ko, mu yƴayƴanmu aure za mu yi musu" kalaman nan ya sa ta kalli sunan mai aikowa abun mamaki se ta ga macece da hoton kan shafin ya nuna babba ce.

"wannan da zan ci karo da ke se na zane miki jiki mara tarbiyya kawai"

Haka na dinga bin su, raina na ɓaci, ina mai cike da-na-sanin wallafawa. Yadda mutanen da ba su sanni ba ke aibatani da iyayena ya sa na fahimci ashe dama mutane ke jira ba wai se mace ta zama ballagaza ba.

Bacci ɓarawo ne ya sace ni, don gaba ɗaya ji na yi zagin zai bi ni har makaranta tun da na ajiye wayar kuwa ban sake ɗagata ba.

Ko da asuba ta yi an kalli bidiyon sau dubu talatin da takwas tunanin goge bidiyon na yi, ko ma na rufe shafin gaba ɗaya.

Kamar an tsikare ni, kawai na sake leƙa kwamen sekshan, anan na ci karo da abun da jiya ban kula ba, yadda mutane ke kare ni a kasan wainda su ka aibata ni.

"mene aibun kalamanta, kun fi so ta fito ta na ballagazanci"

"a haka kuma za ku ce ku sai likitoci mata za su duba matanku alhali ga yadda ku ke ma mata masu neman ilimi."

A haka na dinga bin kwamen din, tabbas ga ma su zagi har sun fi na jiya, sai kuma ga masu ba ni kwarin guiwa da ƙarfafa ni.

A nan na samu sabon ilimi cewa sashin kwamen ba wajen da za ka maida hankali a masu zagi da aibatawa ba ne, waje ne da ake ƙarfafa ma mutum guiwa har ma a samu ilimi.

A take na rubuta kwamen na ce

"Raayi na ba laifi ba ne, in dai kuna da damar samun na ku raayin toh ni ma ina da shi, in nawa ya saɓa maka toh ka kyautata kalamanka" na liƙa shi a sama.

Ina yin haka na sake samun wani kwarin guiwa, tsoron da na kwana da shi ya tafi, saboda na fahimci shiru ba shi ne mafita, sannan bai kamata hayaniyarsu ya hana ka ba don dai yanar gizo bata zo don ta tafi ba.

Tsananin azaba da yunƙurin fitar da abin da ke cikina suka sa na rusa ihun da na ji tamkar zan bar duniyar. An ce idan mutuwa ta zo, mutum kan ga fuskar waɗanda ya fi ƙauna suna giftawa. Ni kuwa, fuskar Sammani ce ta fara bayyana; ba don ƙauna ba, sai don baƙin cikin da ya yi min a zuciya. Wani zafi mai tsanani ne ya keta ta ƙuguna. Mummunar ƙara na kwarara a lokacin da jaririn ya faɗo duniya. Galabaitar naƙudar kwana uku ta sumar da ni.

Na farka na gan ni ni kaɗai a kan gadon asibiti. Wata malamar asibiti ta shigo riƙe da jariri a shuɗin tsumma. "Ga abin da kika haifa," ta faɗa tana wani lallausan murmushi. Ji na yi ina ma ƙasa ta tsage na shiga. Na kasa miƙa hannu na karɓe shi. Hawaye masu zafin gaske suka gangaro kan fuskata, tausayin kaina da na wannan tsumman jaririn ya baibaye ni.

A duk lokacin da mahaifina ya yi min faɗa a kan kwaɗayi, nakan ji jikina ya yi sanyi. Sai dai da zarar ya fita, mahaifiyata takan karkatar da hankalina, tana cewa, "Mace kyakkyawa ai jarinta yana jikinta, mahaifinki ci gaban baya ne." Wannan gubar da ta dasa a raina, ita ce ta jefa ni a ragaumar Sammani.

Wayar da Sammani ya saya min, ashe ba kyauta ba ce; tarko ne. Muka fara tattaunawa a shafukan sada zumunta. Cikin ruɗi da makantar soyayya, na fara tura masa saƙonnin murya da hotuna. Bai tsaya nan ba; ya yi amfani da gata da kyaututtukan da yake ba ni wajen sanya ni tura masa hotunan tsiraicina. Ban sani ba ashe yana ɗaukar dukkan hotunan a matsayin makami (screenshots). Wayar da na ɗauka wayewa ce, ta koma sarƙar da ta ɗaure ni.

Lokacin da na gane ina ɗauke da juna biyu, maganar da muka yi ta ƙarshe ita ce ta fi kowace muni. "Zainabu! Idan na ji sunana a bakinki, to kin fi ni sanin abin da zan saki a yanar gizo. Zan watsa hotunan tsiraicinki duniya ta gani!" ya furta yana nuna ni da yatsa.

Tsoron cin mutuncin yanar gizo da tunanin yadda hotunana za su yaɗu a duniya suka sa na rufe bakina. Na kasa faɗa wa iyayena sunan wanda ya yi min ciki don gudun abin kunya.

Amma yanzu, yayin da nake kallon fuskata a jikin wannan jaririn, na fahimci wani daci: Yin shiru bai kiyaye min mutuncina ba, sai ma ƙara ba abin kunyar damar wargaza rayuwata da ya yi. Ba zan ci gaba da zama baiwar barazanar yanar gizo ba. Zan fasa ƙwai, zan tona asirin Sammani a gaban iyayena da hukuma koda kuwa zai watsa hotunan. Nadamata za ta zama garkuwa da darasi ga sauran yan mata, domin su gane cewa sirrin wayoyinsu na iya zama makamin halakarsu idan ba su yi taka-tsantsan ba.

Hassana Muhammad Lawan daliba ce kuma marubuciya daga garin Potiskum a jihar Yobe, wadda ta kware wajen rubuta gajerun labarai. Ta yi karatun share fagen shiga jami'a a Kwalejin Horas da Malamai da ke garin Potiskum inda ta karanci Ilimin Kula da Gida. A yanzu haka, ta samu gurbin karatu a wannan kwaleji inda za ta karanci fannin Kasuwanci (Marketing). Babban burinta a rayuwa shi ne ta zama shahararriyar marubuciya kuma 'yar kasuwa.

Poetry...

Ya Ubangiji



Ya Ubangiji,
Ka cecemu daga cin zarafin da ke zuwa
A surar ra'ayoyi
Daga mutane wanda suke
Raunta mata ba tare da sun
Taba zama a wuri daya ba
Ameen
Yanzu wayoyi sun zama
Dakuna na biyu da mata suke kukan zuci
A sirrance – Kamar yadda suke ganawa da Ubangiji.
Ko wace ranar da wata yarinya ta hau yanar gizo
Kamar shiga gidan kwalba ne
Da yake haska farfashewa
Kuma bai kare komai
Wuri ne inda sunaye suke zama
Abar tuhuma, in da jukkuna suke zama abun muhawara
In da ake wasa akidoji da harsuna
Kamar sababbin wukake.

Taku ɗaya, kuskure ɗaya da kuma kalma guɗa ɗaya tak kan iya sauya rayuwar ka daga fara kalar madara zuwa baƙin da ya fi na duhun dare. Rayuwata tayi sauyin sheƙa daga gidan gara na tsinci kaina a na zago sakamakon takun da nayi, tsalle ne guda ba kuma irin masu gasar tsalle kan yi ba balle a ce naje hangen abinda babba ke hangowa daga zaune. Ba ma fa a zahiri bane nayi tsallen, a bayan fage ne cikin tsakiyar dare a kan fuskar waya ta.

Na san za kuyi mamaki in nace muku wai kalmomi hamsin ne kacal suka kawo ni inda nake a yanzu, amma kuma ai ba abun mamaki ba ne ba. Duk da in zaku tambaye ni ba na ce ga abinda ya ja ni na yi rubutun ba, kuma dai ban son laluben nema don ba abu ne da zan so gani ko sani ba. Abu ɗaya na sani shi ne na biye abinda ake yayi ne a zamanin nan wato "Tirandin" ba tare da na san cewa ba kowa ni yayi ba ne na kowa da kowa, don fa in wani yayi rawa aka watsa kuɗi wani in yace zai yi…? Ban kuma ce fa ba'a yi a wanye lafiya ba, don da fari na zaci cewa ina ɗaya daga cikin masu yi su sha hankalin su kwance wai tsumma a randa sai dai kuma kash...

Na san kuna nan kuna tunanin me na aikata haka ko? To bari in baku satar amsa. Don nayi tirandin ɗin da nake son yi har ma fiye da wanda na so ɗin, don labari na yana ɗaya daga cikin wanda yayi tashe a kafar sada zumunta ta X da Instagiram. Bai kuma tsaya a nan ba sai da ya zagaya Fesbuk har a dandalin Tuktok, kai ko baka a kafafen sada zumunta ma ina tabbatar maka a shekarar da ta gabata to labarin ya ishe maka a dandalin kunne ya girmi kaka.

Shin kun tuna da labarin wata yarinya ƴar gidan Sina? Wanda aka fara daga Tuktok ta ƙare a X? Toh shi ne dai yake riƙe da nawa labarin. Wanda ya faru a wata yammacin ƙaddara da ta kai ni ga daren nadama, ina kwance kan katifata ina kallon gajerun bidiyo a Instagiram na ci karo da nata. Bidiyo ne na irin matan da Allah ya musu arziƙin ƙiba ba ƴar kaɗan ba a wurin biki tana rawa, da sauri na garzaya sashen sharhi inda na duba duk babu wani abun ƙi a abinda suke kwament kowa sai Ma Sha Allah yake ta fadI.

Kun san Allah ɗaya ne ko? Wallahi ko kaɗan abun bai min daɗi ba, na san hakan zai kuma ba ku mamaki amma ni haka nake. A duniya na tsani in ga an yi fos a kafafen sada zumunta kuma ya zama babu wani rikici a filin sharhi sai sam barka, inda a take zuciyata ta raya mini tafiya Tuktok don na san zan ga abinda nake nema. Zuwa na ke da wuya ko abinda na fara cin karo da shi kenan, don can dai filin sharhin babu mai fadin abun arziki kowa sai sukan halittar yarinyar nan yake yi. Daga masu kiran ta buhun masara sai wainda nasu ya fi wannan muni abu dai ba kyan gani, duk wani mutum mai hankali in ya ga sharhin nan sai ran shi ya ɓaci amma ban da ni don daɗi na ji har cikin raina. Kuma maimakon in bar shi a inda na gani tunda na samu abinda nake so ko? To ba hakan nayi ba don kai tsaye na zabga sikirinshot na tafi da shi Fesbuk don kun san mutanen mu na can ba su gani sai sun tanka. Kai na tsaye na kai shi shafina na yi rubutun kalmomi hamsin ɗin da na gaya muku, wainda duk kalmomi ne na ɓatanci da izgili ga halittar ta. Cike da farin ciki nayi bacci a daren ranar don na samu abinda nake so.

Washegari ko da sassafiya na kunna data na nufi Fesbuk, ina gaya muku abinda dai na neman na don ko na tarar saƙo na na dare ya samu karɓuwa fiye da zaton mai tunani. Inda da yawan mutane suka taya ni ƙarasa abinda na fara, ɗaiɗaiku ne ke sukar abinda na aikata amma tunda kwalliya ta biya kuɗin sabulu sai nayi tsaki na kashe datar nayi shirin tafiya makaranta cike da farinciki mara misaltawa. Ko a can ma zancen muka dinga yi da abokan karatu na inda suka dinga sukar ta amma iyakacin su bakin su ba su taɓa kai irin abun nan midiya ba. Don duk wani fos da za'a yi a filin sada zumunta su kan yi sikirinshot su tura shi tsakanin mu in aka haɗu a tattauna amma fa ko a filin sharhi ba zaka taɓa jin tarin su ba, wannan ƙarfin halin sai ni. Da aka tashi kuwa tun a hanya na kuma kunna data don ba zan iya jira har in isa gida ba, nan na ga sabbin sharhi sun daɗu kuma na yanzu masu zagi na sun fi masu yabo na yawa har da wani da ya yi barazanar sai na ga abinda zai biyo baya ko kaɗan kurarin shi bai ɗaɗa ni da ƙasa ba balle ya kayar sai ma tabbatar masa da nayi cewa ba abinda zai iya yi. Bai ko kuma tanka ni ba, nima kuma ba ta shi nake yi ba don na sanin mai amfani da K.D_Scribbles abu ne mai matuƙar wahala don ba ma wanda ya taɓa ganin hotuna. Sake yin abinda na fi ƙwarewa wato sikirinshot na yi nayi sabon fos cike da izgili gare shi da tsokanar shi kan yayi abinda zai iya, wannan fos ko ya ja cecekuce a daren ranar don shi da masu ganin aibun abinda na aikata sai tare masa suke

suke nima mutane na suna goyon bayana. Wallahi a ranar har ji na nayi kamar wata sarauniya da masu take mata baya, sai dai mutumin yayi mugun ɓata min rai don ban ga dalilin da zai saka ba zai yi abinda ke gaban shi ba wai ina ruwan shi da ni ne ma? Haka nayi bacci cike da baƙin ciki karo na farko da naji ina ma zan san waye shi a zahiri sai mu yi faɗan baki da baki ai zai fi armashi.

Da asuba ko da na farka na tadda kira kusan goma ko fiye wainda na rasa, wanda abu ne mai matuƙar mamaki don sai in fi sati ba a kira ni a waya ba ma balle har ace na rasa kira fin goma. A take ƙirjina ya buga da mugun ƙarfi tsoro ya mamaye min zuciya, ƙarin tsoron kuma sai da wani kiran ya kuma shigowa cike da firgici na ɗaga Lara ce ɗaya daga cikin ƴan uwan mu. Da masifa ta balbale ni tana tambaya ta me na aikata haka? A tsorace nake tambayar ta abinda ya faru sai dai maimakon amsa sai cewa tayi in duba shafin wata fitacciyar mai rubutu a Instagiram. Da sauri na tafi inda na haɗu da abinda ya kuma sage min guiwa wato ganin ana tallar nema na ba kuma iya nan ya tsaya ba har da Hotuna, sunana na gaskiya har ma da sunan da nake amfani da shi a midiya duka ga shi nan.

Ai sai na zame kan katifa ina jin kamar an juye min bokitin ruwan sanyi a ka lokacin bazara, waye zai min haka ne? Waye ma ya sanni da har zai binciko ni da komai nawa haka? Kuma fa ba iya wannan ne abun tsoron ba har da sammacin kotu gashi nan kowa yana gani ahalin Sina suna ƙara ta kan cin mutunci da tozarci har ma da tsangwama. Ai a take cikina ya fara juyawa da sauri na jefar da wayar na faɗa bayi, ina yi ina kuka don na san ƙarshe na ya zo haka na ɗuka dai har sai da ƙafafuna suka sage kafin na koma ɗaki na kwanta kan gado Kafin kace kwabo zazzaɓi ya rufe ni rigijib haka na dawo na kwanta ga ciwon ciki ga kuma zafin jiki ga kukan zahiri da na zuciya, musamman da wayar tawa ba ta daina tsuwa ba ga shi ina da gwaji ranar a makaranta amma ina tsoron fita don na san za'a iya kama ni zama na a gida shi ne mafi alheri tunda dai ba su san ni ba.

Ina a kwance Mama ta shigo tayi mamakin gani na ko da ta tambaye ni abinda yake damu na cewa nayi bani da lafiya ne, sosai ta tausaya min ta bani abinci da magunguna sai dai ban ko iya cin abincin ba na dai sha maganin da na tabbatar ba aikin da zasu iya yi. Ina a wannan hali ban san ya aka yi bacci ya ɗauke ni ba sai da Mama ta tashe ni wai nayi baƙuwa, duk da dukan uku da ƙirjina yake yi haka na fita a saɓule na tarda baƙuwar fuskar da ban taɓa gani ba sai dai na daure na ɗofana kan hannun kujera ina gaishe ta. Amsawa tayi tana ƙare min kallo kafin tace " ke ce Kande Dauda?".

Salati da sallallami na fara a raina don na san ta faru ta ƙare wai an wa mai dami ɗaya sata sai dai na daure nace " Ni ce, lafiya dai ko?".

A take murmushin kan fuskarta ya ɓace ɓat ta miƙe tsaye zuwa gabana ta zaro hannayen ta daga hijabi, karaf idanu na suka faɗa kan ankwa ta kaɗa shi kan fuska ta tana cewa "Kin shiga komar hukuma" faɗin nata kuma yayi daidai da fitowar Mama daga madafa tana tambayar abinda yake faruwa. Ni dai nayi shiru kamar wacce ruwa ya cinye sai kallon-kallo nake yi daga jami'ar farin kaya zuwa ga Mama dake bina da kallon tuhuma baki na yayi nauyi harshe na ya ɗaure sai ƙyafta idanu nake yi kamar ɓera a buta.

Yayin shiga yanar gizo



Ta shiga, kamar addu'a mai haske
fiye da madubi
A nan, haske ce
Kafin su yi yunkurin disashe ta
da yatsun su
Da kalmomi masu kaifi

"Turo min”
"Nuna min”
"Mu gani a kasa"

A nan kaifin harshe ya yi tasiri kan ta
Kamar wadda aka ɗauke.
Sai ta zama kamar jita-jita
A tabbace.

Amma yanzu ci take kamar wuta
Da ba za a iya kashewa ba

Poetry...

Ke mace ce



Allon na'urata wata ƙasa ce mabambanciya,
Inda biranenta suka koma karkami a duniya,
Suna bayar da ciwo da raɗaɗi mai ratsa zuciya,
Fiye da dukkan ɓoyayyun taskokinmu na asirriya,
Waɗanda muke binnewa a rumbun hotunanmu don kariya.

A cikin wannan ƙasa tawa ta zahiri da magagiya,
Babu wata taswirar nuna hanyar Aljanna gaba ɗaya,
Kamar yadda babu taswirar gano gurbin ciwo a zuciya,
Duk da haka, ciwo yakan rufe fuskarsa ya yi shigar burtu ta wata hanya,
Ya kuma bayyana kansa a matsayin "ɓoyayye" mara son gaskiya.

Wata irin arangama ce mai cike da firgici a ɓoyayyiyar hanya,
Wadda ke matuƙar tsoron fuskantar gangar jiki a bayyane gaba ɗaya,
Amma duk da haka takan yi sulalu ta samo mafita ta tata hanya,
Domin ta farfasa ruhin ɗan-adam ta mayar da shi gunduwa-gunduwa ta kowace hanya,
Sannan ta jefa shi a wani baƙin kurkukun da babu mantuwa har abada a duniya.
Ke mace ce

Poetry...

Ke mace ce



A cikin ƙasa mai cike da ɓata gari
Wurin da tsana da ɓacin rai ke jan ragama
In da ihunka ba abinda zai kawo
Saboda kowa ya yi shiru yana kallo

A nan, buri ke ɓacewa kamar yadda hasken rana ke faɗuwa
Yayin da duniya ke cigaba shiga ruɗu
Wanda ke janyo ɓacin rai ga ruhina
Amma ba wanda ke nuna damuwa

A cikin ƙasar da ke kallon "shi" a matsayin mai iko
Yayin da ake ma "ita" kallon marar iko
Dole in tsorata saboda ban san ya za a kira ni ba a lokaci mai zuwa
Dole in tsorata saboda ban san yadda sunana zai karaɗe wurare ba
Yadda kallo zai min illa amma ba zan iya kokawa ba
Saboda kawai ni mace ce
Amma ba ka tunanin mahaifiyar da ƙanneka mata
Da mutuncin gidan da suka fito?

A irin haka aka rufe min baki a yanar gizo
Ga duk wani buri na da mafarki na
Saboda wasu sun tura rayuwa ta cikin ƙunci
Saboda dole in daidaita rayuwata yadda suke so domin in samu sukuni

Amma sun mance cewar yarinya ce ni cikin damuwa
Amma a haka ake so in yi shiru
Dole in koyi rayuwa haka idan ina son samun cigaba

Raunuka Marasa Hannaye



Ta fara fada mana akan raunukan da idanuwa basu gani, masu nauyi kaman kacha a teku

Saboda an wurgo kalamai, duk da ba hannuwa, wadanda suka karya mata kasusuwa

Ta hanyar hasken fuskar waya da daddare, aka yi mata Rashin daraja

Muryoyi dubu, suna ihu cikin Rashin tausayi, suna boye fuskokinsu

Suka sassaka tsanarsu ta waya, suka bace cikin duhun dare

“Waye ya bangaje ni haka”, yarinyar ta tambaya, “shi ba habbu ba, ba wuka ba, amma sai da na tsiyaye ta ciki”

Sai hikima ya amsa, cikin lumana, “harshe zai iya yin raunin da zai bar tabo”

Saboda tawada da kyamara sun hada kai wurin rura wutan da ba’a gani

Ga zukata sun gaji, sun yi jina jina daga yakin a yanar gizo

“Mike”, yace, ya ke me wutan ciki, kin wuce su ba ki suna”

Saboda ita gaskiya ta fi dawwama aka zanen karya, kuma haske na dawwame a zuciyarki

Kar mu bar inuwarsu su kaskanta ki, ko kuma muryarsu

Saboda ko ba hannuwa masu duka, ruhinki a tsaye yake – a mike, cikin karko.

Poetry...

Kawai Ni Mace Ce



Don kawai ni mace ce a filin sadarwa,
Mai haɗe da intanet da mafarkai marasa ƙarewa,
Hakan bai mayar da ni abin zolayarku ba wajen wulakantawa,
Kuma kalmominku ba za su datse fukafukina ba wajen tasawa.

Na zo nan ne domin in koya, in kuma samu bunƙasawa,
In wallafa fasahata don duniya ta gani tana jinjinawa,
In rubuta labaraina, in raba haskena mai ci gaba da haskawa,
In samo 'yan'uwa mata da za su sanya ruhina ya samu nutsuwa.

Don kawai ni mace ce,
Yarinya ƙarama, mara sani, sannan mai son ganowa,
Wannan bai nufin munanan shafukanku masu gurɓatawa,
Su yi amfani da damar wajen sanya kamalata salwantawa.

Cewa suka yi "Kawai latsa", "kawai amince", "kawai yi wasa abin burgewa",
Amma kowace "kawai" da na yi, tana wani yanki nawa ragewa,
A tsakanin dariyarsu ta ƙeta da maƙaryata masu yaudarawa,
Na rasa wani ɓangare nawa da na kasa gane siffarsa wajen tantancewa.

Don kawai ni mace ce,
Mai sauƙin amincewa da mutane, kuma mai burin ɗaukakawa,
Hakan ba zai mayar da ni mazubin zambarku ba masu damfarawa,
Ni fa ƙaƙƙarfa ce, ba rarrauna ba, kuma jaruma mai matuƙar dagewa.

Kun zaci za ku iya yi mini wayo cikin dabarar cuwa-cuwa,
Ku rufe fuskokinku a bayan sunayen bogi kuna cutarwa.
Amma na ɗauki darasi... a yanzu na gane ina lura(wa)...
Shirun nan naku da shirye-shiryenku na muguntawa,
Ba za su iya danƙwafar da macen da ta gano wutarta ba tana rurawa.

Don kawai ni mace ce,
Hakan bai nufin ba ni da matsayi a nan, kawai dai na dinga shiryawa,
Wannan sarari, wannan duniyar intanet... tawa ce ni ma a matsayin mallakawa,
Domin in yi mafarki, in gina ayyuka, kuma in sabunta tawa rayuwa.

Abinda ya fara zuwa raina lokacin da wata lamba da ban sani ba ta bayyana a wayata shi ne ɗan damfara tare da tunnin ɗaya daga cikin irin kiran nan ne da ake yi a tambaye ka lambar sirri ko a ce bankinka na da matsala.

Na yi dariya saboda tunanin, saboda yaushe ɗan damfara ya taɓa kirana da irin wannan magana? Gaskiya bai taɓa faruwa ba, amma kamar kowanne ɗan Najeriya, na ɗauka wannan zai zama lokacin.

Ina cikin wannan tunanin sai wani tunani ya ratsa zuciyata ko dai wata dama ce ta aiki? Ɗaya daga cikin ayyukan da na nema tun farkon shekara.

“Hello?”

Na ɗaga wayar na sanya kusa da kunne, zuciyata na bugawa da ƙarfi kamar ina zaman jiran wannan labari mai daɗi? Idan hirar aiki ce, shin a shirye nake? Ko kuwa irin wadda ake yi a take ce, irin waɗanda na taɓa yi a watan da ya gabata na kuma na kwapsa?

Tunani na ya katse da muryar da ta fito daga ɗaya ɓangaren.

“Salama Alaikum.”

Ba mai ɗaukar aiki ba ne, kuma ba irin muryar rikodin ɗin damfara ba ce sai dai ko sun canza dabara.

Tsammani na sai ya ragu, fargaba ta fara shigowa a hankali, daga baya ta ƙaru. Muryar tana ɗauke da wani irin amo na gaggawa kamar ni nake ɓata masa lokaci. Ko wani ya rasu? Ko kuwa masu garkuwa da mutane ne?

Na zauna ina saurare dai..

Muryar ta yi kamar ta yaro ɗan kimanin shekara 16 ko 17.

“Salama Alaikum.”

Wannan shi ne karo na uku.

“Wa’alaikumus Salam, wa ye?”

“Wa ye?”

“Ba kya ji ne? Na ce Salama Alaikum.”

A wannan lokaci na fara jin haushi. Ƙarfe kusan goma na dare ne, kuma bayan gajiyar yini, ban da lokacin sauraron baƙo, balle wanda bai san darajar lokaci ba.

“Ni kuma na ce waye?”

Sai shiru ya biyo bayan yanke kiran. Na zauna ina kallon waya cikin mamaki da haushi. Wayata ta sake ƙara. Na ɗaga.

“Salama Alaikum.”

Na yi shiru. Shin wannan mutum ya cancanci amsa kuwa? Na ji wata muryar a cikin wayar tana raɗa:

“Wai ba a amsa wa ne? Me ake cewa?”

Ba kiran gaggawa ba ne. Ba kuma kiran fansa ba ne. Yara ne kawai masu ɓata wa mutane lokaci, kuma ni ce na zama wanda suka samu.

“Ku baku da hankali ne? Da daɗaɗɗen daren nan sai ku dinga damun mutane da kira? Haba!

”A wannan karon ni na yanke kiran.

Ƙarfin da ya cika jikina ya fara raguwa. Sai ɓacin rai da ke damuna sosai Ƙarfe shida na safe ma wayata ta cigaba da ƙara. Na kwana ina aiki har bayan sallar asuba, kuma ban daɗe da yin barci ba. Kiran ya dame ni, kai na kuma ya sara da ciwo.

Na ɗaga wayar.

“Salama Alaikum.”

Na yi nishi cikin takaici. Ban amsa ba, kuma ban yanke kiran ba. Na sake shiru na bar wayar a gefe.

Na saurari shiru. Bayan mintuna biyar, kiran ya yanke. Sai wani ya shigo. Na ɗaga, har yanzu shiru.

Ana ci gaba da haka sau da yawa, amma zuwa kira na uku, na fahimci cewa wanda ke can ya fara jin haushi sosai. Wannan ya sa na ƙuduri aniya.

Na yi murmushi—da sun gaji da tuni sun daina kira.

“Ke, nace Salama Alaikum.”

“Wai ba a amsa wa ne?”

“Durun uwarki, nace baza ki amsa bane?”

Zagin ya taɓa ni. Ba wai don ban taɓa ji ba, amma saboda na san irin inda yake fitowa—wani irin lalacewar tarbiyya ne haka.

“Ke zanci mutunci ki, yar shegiya, mara kunya.”

Abun da ciwo yara irin waɗannan suna irin wannan zaagin. Amma ramawa zai zama kamar na koma kamar su kenan..

Na buɗe manhajar Truecaller amma babu wani bayani. Sai na rubuta: ɗan damfara

Mutumin nan ba shi da abin yi. Ku yi hattara da kiransa.

Sai na toshe lambar.

Na ɗauka komai ya wuce. Har kwanaki biyar suka shige. Amma a rana ta shida, wayata ta sake ƙara.

“Salama Alaikum.”

Na sake yin shiru.

“Shegiya, yar iska.”

“To wallahi baki san wa kike wasa da shi ba.”

Ban ɗauki barazanar da muhimmanci ba.

Sai na ji wata muryar:“Me ta ce?”

“Kyale munafukar yar durun uwa. Idan ita bata san mu ba, mu ai mun san ta.”

Kiran ya yanke.

Wannan kalmar ta ƙarshe ta tsaya min a zuciya. Shin da gaske sun san ni?

Ni ba wata mashahuriya ba ce. Ni dai yarinya ce , ba ma mai yawan fita ba wurare ba. Idan zan fita sai na zaɓa wurin zuwa.

Sai na gane wata kila daga yanar gizo suka samo lambar.

Kamar yawancin matasa, ina amfani da kafafen sada zumunta sosai—X, Facebook, LinkedIn, Snapchat da sauran su domin nuna aikina. Kuma na saka lamba ta a shafi na domin a tuntuɓe ni domin samun dama ko wani aiki.

Sai na fara jin tsoro. Shin na fallasa kaina ne?

Na tuna yadda nake saka wuraren da nake a hotuna, har ma ina wurin a lokacin.

Me na yi musu? Me na faɗa? Me na rubuta? Ban sani ba, kuma ban so sani ba.Na yanke shawara biyu: toshe lambar, sannan na cire lambata daga shafina.

Na gane ba zan iya yarda da kowa a yanar gizo ba. Kowace murya na iya zama kowace fuska.

Na rage ɗaga kiran lambobin da ban sani ba, musamman waɗanda ba su da suna a Truecaller.

Amma har yanzu, duk lokacin da wayata ta haska da lamba baƙuwa, zuciyata tana tsorata tana jin ɗarr.

Ba kira ba ne kawai yanzu.

Tunawa nake cewa duniya na kallon mu ta cikin abubuwan da muke ɗorawa a shafukan sada zumunta.

Hotuna



Build-Tech Project

Tech. Ethics. Solutions.

ISBN 978-978-68-7621-4